**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**

**A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto**



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)

**DOI:** https://doi.org/10.65760/kassu.i1.4 **Website:** www.ssu.edu.ng |**Issue 1** | **April 2025**|

# Gurbin Sana'o'in Gargajiyar Hausawa a Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Aminu Ibrahim**

Sashen Harsunan Nigeriya, Jami'ar Umaru Musa Yar'adua, Katsina

**Corresponding Author: Aminu Ibrahim** ibrahim.aminu@umyu.edu.ng
Lambar Waya : 08067795891

**Tsakure**

Babbar manufar maƙalar ita ce fito da sana'o'in gargajiya na Hausawa, waɗanda Kassu Zurmi ya taskace a cikin waƙoƙinsa tare da duban yadda shi makaɗin ya kalle su a cikin waƙoƙinsa, kuma a fito da gudummuwar da suke bayarwa wajen inganta tare da bunƙasa tattalin arziƙin Hausawa. An yi ƙoƙarin fito da dangantakar da sana'o'in da aka ambata a cikin waƙoƙin suke da shi da kuma yadda hakan yake samar da kyakkyawan yanayi na cuɗanni-in-cuɗe-ka a tsakanin sana'o'in na gargajiya. An yi amfani da hanyoyi da dama wajen tattara bayanan da aka yi amfani da su wajen gina wannan maƙala. Hanyoyin sun haɗa da, yin hira da masana, musamman na waƙoƙin baka da nazarce-nazarcen littattafai da kundayen da magabata suka rubuta a kan waƙoƙin Kassu Zurmi. Har wa yau, an saurari waƙoƙinsa da aka naɗa a faya-fayen sidi na rediyo da na talabijin. Binciken ya gano yadda Hausawa suka ɗauki sana'o'insu na gargajiya da daraja, kuma abin dogarau wajen neman na kai da kare mutunci. Haka kuma, Hausawa na matuƙar alfahari da sana'o'insu na gado, kuma suna kare martabarsu a duk inda suka samu kan su ba tare da jin tsoro ko fargaba ba.

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Wannan maƙala ta yi duba ne a kan matsayin da sana'o'in gargajiyar Hausawa suke da shi a cikin waƙoƙin Makaɗa Kassu Zurmi. Wannan shahararren mawaƙi ya ba sana'o'in Hausawa wani matsayi na musamman, kuma ya yi amfani da su a matsayin tubalai da ya gina waƙoƙinsa da su. Har ila yau, Makaɗin ya fito da hotunan wasu daga cikin sana'o'in gargajiya da Hausawa suka gada inda ya fito da su tare kuma da nuna darajarsa ga al'umma. Akwai tarin sana'o'in da Kassu Zurmi ya zayyano a cikin waƙoƙinsa tare

bayyana tushensu da kuma yadda ake gabatar da wasu a aikace. Batutuwan sana'o'i a cikin aikace-aikacen fasahohin Kassu Zurmi, su suka tabbatar da sana'o'in da ya gabatar a matsayin na asali kuma masu tushe a ƙasar Hausa. Har wa yau, ya ƙara fito da bayanai na yadda mutane suka rarrabu ta fuskar yadda sana'o'in suka rarrabu a tsakanin al'umma, kuma ya fito da tsari na zaman tare da masu sana'o'in ke da shi, wanda yake tamkar ruhi ko ginshiƙin zaunar da mutane a waje ɗaya don gudanar da rayuwa. Kowane mai sana'a, musamman ɗan gado kan nuna wasu al'adu na kare martabar sana'ar da aka san shi da ita a duk inda ya same kansa. Kamar yadda waƙoƙin Kassu suke nunawa, za a ga da wasu fitattun sana'o'in gargajiya ya gina tubalai da ya yi amfani da su wajen gina waƙoƙinsa. Kassu Zurmi makaɗin maza ne, domin 'yan farauta yake yi wa waƙa, kuma tarihi ya nuna cewa, kakansa mahauci ne don haka ba abin mamaki ba ne don an samu nason sana'o'i a cikin waƙoƙinsa.

An yi amfani da hanyoyi da dama wajen gudanar da wannan bincike don a cim ma manufa da kuma fito da cikakken hoton aikin. Waɗannan hanyoyi sun taimaka ƙwarai tun daga matakin neman bayanan farko har ya zuwa kammaluwar aikin. Daga cikin hanyoyin da aka yi amfani da su akwai yin hira da masana, musamman na waƙar baka. Wannan hanya ta taimaka wajen fito da tarin bayanan da suka taimaka wajen ginuwar aikin. Baya ga su, an samu zantawa da wasu rukunnan mutane, musamman waɗanda suka riski zamanin da Kassu Zurmi ya rayu da iyalinsa da suke raye a yanzu da kuma wasu dattawa masu sha'awar waƙoƙinsa. An yi amfani da bayanan da aka samu daga gare su wajen tabbatar da wasu fitattun batutuwa tare da kore wasu zantukan da ba su da inganci. An kuma nazarci ayyukan magabata da suka haɗa da kundayen bincike da aka gabatar a makarantu daban-daban da littattafai da kuma maƙalu, wanda hakan ya taimaka wajen samo wasu sahihan bayanai masu tushe da nagarta da suka agaza wajen daidaita bayanan da aka yi amfani da su wajen gina aikin tun daga farkon farawarsa har ya zuwa ƙarshe. An kuma yi amfani da hanyar sauraron fayafayan sidi da suke naɗe da waƙoƙin Kassu Zurmi wajen nazari da fashin baƙin wasu ɗiyoyin waƙoƙin da Kasuu Zurmi ya yi a lokacin da yake raye. Waɗannan hanyoyi da aka zayyano sun taimaka wajen tabbatar da nasarar da aka samu na wannan aiki.

## 2.0 Taƙaitaccen Tarihin Makaɗa Kassu Zurmi

Makaɗa Kassu Zurmi, makaɗin maza ne, kuma cikakken sunansa Abubakar Amadu. 'Yan tauri yake yi wa waƙa. Tarihi ya nuna cewa, Makaɗa Abubakar ya samu wannan laƙabin ne na Kassu daga ranar da aka haife shi. An haife shi ne a ranar kasuwar wani gari da ke maƙwabtaka da garin da aka haife shi. A lokacin da aka haife shi babu kasuwa a garin Magarya, watau garin da aka haife shi, amma akwai kasuwa a wani babban garin da ke kusa da Magarya da ake kira da Dunfawa. Dunfawa gari ne da ke cikin masarautar Mawarƙi da ke cikin ƙaramar hukumar Zurmi. Ya samu laƙabin mai kasuwa daga ranar kasuwar Dunfawa. Da ya tasa, sai aka gutsire sunan daga mai kasuwa ya zuwa Kassu. Wannan suna na Kassu ya yi tasiri a rayuwarsa har ya kai ga ɓatar da sunansa na yanka, watau Abubakar, sai aka riƙa kiran sa da makaɗi Kassu Zurmi. Ba a samu takamamman yawan shekarunsa na haihuwa ba, amma sahihan bayanai sun tabbatar da cewa shi Bagobiri ne. An ce asalinsa mutumin garin Kurawa ne ta ƙasar Sabuwar Birnin Gobir. Kakansa da ya haifi mahaifinsa, watau Gandau, tarihi ya nuna cewa mahauci ne. Ya yiwo ƙaura daga garin Kurawa ya zuwa Dunfawa. A garin Dunfawa kakan Kassu Zurmi, watau Gandau wanda ya haifi mahaifinsa ya zauna. A garin Dunfawa Gandau ya zauna ya riƙa sana'ar fawa, kuma ya shahara a a kanta. Tarihi ya tabbatar da cewa har sarauta sarkin fawan Dunfawa ya yi. Har ila yau, tarihi ya bayyana cewa Kassu Zurmi ya gaji sana'ar kiɗa

ne daga wurin mahaifinsa, watau Amadu. Amadu makaɗin duma ne irin na girke. Yana yi wa manoma da mahauta da kuma 'yan bori kiɗa. Da wannan nau'in sana'ar kiɗa aka san mahaifin Kassu. Mahaifin Kassu Zurmi ya taso daga Dunfawa ya koma garin Magarya. A garin aka haifi Kassu Zurmi aka kuma raɗa masa suna Abubakar. Amadu ya sake tashi ya matsa ya zuwa Kadawa. Daga baya kuma, Amadu ya sake tashi daga Kadawa ya koma Magarya. A garin Magarya mahaifin Kassu ya rasu. Ko da Amadu ya sake komawa Magarya, Kassu Zurmi bai bi shi ba, domin ya yi zamansa ne a Kadawa. Tun yana ƙarami aka fara ganin abubuwan fasaha a tattare da shi. Da haka ya tashi har ya zuwa lokacin da ya fara kiɗan bori da duman da ya gada daga wajen mahaifinsa. Akwai wani mafarauci da ake kira da Sarki Bahago, wanda tarihi ya nuna cewa, asali shi mutumin Tatika ne, wadda ke gab da garin Magarya, kuma ɗan farauta ne. An ce shi ya sayi wa Kassu Zurmi ganga. Bayan ya sai masa ganga, sai ya neme shi da ya yi masa waƙa ta farauta, wanda daga lokacin ne Kassu ya fara kiɗin farauta[1].

### 3.0 Yara Masu Kaxa masa Kalangu

A garin Gandasamu, Kassu Zurmi ya samu yara masu kaɗa masa kalangu. Gandasamu wani ƙauye ne kusa da Tatika, wanda ke kusa da Magarya da Kadawa. A garin ne wani yaronsa mai suna Dodo yake, kuma yana daga cikin mashahuran yaransa da ke yi masa kiɗa. Bayan shi akwai Shata, sannan akwai ɗan cikinsa da ake kira da Ummaru Kaho. Bayan shi, akwai Sani Ɗagabci da malam Ali mai kaɗa masa zakka. Har ila yau, akwai Shata Maba., amma ba wancan Shatan da aka ambata a baya ba. Ba kiɗin kalangu yake yi ba, yana taka rawar maroƙa ne, watau maroƙin bakinsa ne. Aikinsa shi ne ya yi masa bambaɗanci a yayin da yake waƙa. Da su ya haɗa tawaga, kuma da su ya fara kiɗin tauri. Daga nan ya fara har ya shahara, kuma ya fara fita zuwa wurare a faɗin ƙasar nan.[2]

### 3.1 Tsarin Fasalin Waƙoƙin Kassu Zurmi

Kassu Zurmi makaɗin maza ne, kuma ya yi amfanin da salon kiɗa da kansa, sannan sauran 'yan tawagarsa, kowa na da nasa aiki, amma ba sa yi masa amshin waƙa. Ba a amshi a waƙarsa. Wasu daga ciki na kaɗa masa kalangu wasu zakka, ko kuntuku, wasu kuma bambadanci suke yi masa a yayin da yake waƙa. Shi kaɗai yake waƙarsa, watau shi ke tsara abin sa tare da rera ta kai tsaye. Idan ya zo ya ba da salon waƙar da za a kiɗa masa, idan yaransa suka ɗau hannu, sai ya ɗaura waƙarsa kawai. A wasu lokutta masu yi masa kiɗa suke fara buɗewa da kiɗa, watau sukan fito da kiɗin da suke ganin ya dace da hawa da saukar waƙar da za ya yi. Akwai lokuttan da shi da kansa yake amsar kalangu ya fitar da salon kiɗin da yake so a yi masa. Haka kuma, akwai lokuttan da har tsawata wa makaɗansa yake yi, musamman idan suka kasa yin yadda yake so, watau ya nuna ba haka yake so ba. Wannan kamar wani salo ne da yake amfani da shi wajen bayar da umarni ga yaransa don su yi yadda yake buƙata.[3]

### 3.2 Salon Kiɗin Taurin Kassu Zurmi

Kiɗin tauri, kiɗin maza ne. Kiɗi ne da ake yi wa maza don a tayar masu da tsimi, domin su nuna jarunta a yayin da ake gabatar da kiɗin. Kiɗin tauri kamar na dambe ne, domin abin da ya bambanta su shi ne, ana amshi a kiɗin dambe, yayin da kiɗin tauri, musamman irin

[1] Hira da aka yi da Malam Ibrahim Muhammad Ɗanmadamin Birnin Magaji tare da Muhammadu Sayaya a gidan rediyon Nijeriya na Kaduna FRCN a 31-03-2019.

[2] A dubi tushen bayani mai lamba ta ɗaya.

[3] Hira da aka yi da Malam Ibrahim Muhammad Ɗanmadamin Birnin Magaji tare da Muhammadu Sayaya a gidan rediyon Nijeriya na Kaduna FRCN a 31-03-2019.

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 

ta Kassu Zurmi, ba a amshi, kuma shi kaɗai ke da irin wannan salon. Hamisu Sarkin kiɗa da Garba ɗan wasa Gummi duk ana yi masu amshi idan suna waƙoƙinsu, musamman waƙoƙin da suke yi na 'yan tauri, amma shi Kassu Zurmi ba ya buƙatar amshi. Idan ya tayar da wanda yake yi wa waƙar, ya fara zuga shi, watau yana kambama shi, a wasu lokutta za a ji su waɗanda ake yi wa waƙar sun fito suna kirari, domin kiɗin ya ratsa su, kamar dai yadda ake gani a yayin da yake kiɗa.

**4.0 Ma'anar Sana'a**

Kalmar sana'a ta samo asali ne daga larabci, watau kalma ce da Hausa ta aro daga larabci. Wannan ba wani abin kunya ba ne ga harsunan duniya, domin akan samu aro na kalmomin da suke bayyana wasu sababbin abubuwan fasaha da al'adu a tsakanin harsunan duniya. Kalmar sana'a a Larabce, watau yadda take a asali, ita ce, "Assana'atu"[4]. A Larabce tana nufin, yin hikima ta amfani da dabara da basira wajen sarrafa wani abu ya zuwa wani don amfanin mutane. Idan aka ɗauki ƙarfe a matsayin misali, za a ga ana iya sarrafa ta a cikin hikima da dabara a samar da kayan aikin gida da na masu gudanar da waɗansu sana'o'in gargajiyar Hausawa. Wannan nau'in aikin na juya wannan ma'adanin, watau ƙarfe ko tama, domin ƙera tarin kayayyakin aiki da na amfani don masu gudanar da wasu sana'o'i su samu damar gudanar da ayyukansu, ita ce ake kira da sana'a ga masu gudanar da ta.

Sa'id (2006:387) ya fassara kalmar sana'a da, "Aikin da mutum yake yi don samun abinci." Idan aka yi duba da wannan fassarar, ana iya cewa sana'a hanya ce ta sarrafa wani abu, musamman ta amfani da gaɓoɓin jiki, ya zuwa wani abin amfani don buƙatun rayuwa. Haka kuma, an rarraba sana'o'in Hausawa ya zuwa gida biyar, waɗanda suka haɗa da, sana'o'in samar da abinci kai tsaye da masu samar da mafaka da sutura, da sana'o'in samar da kayan aiki da sana'o'in safara da ciniki da kuma sana'o'in yi wa mutane hidima ko gyara (Alhassan da wasu, 1988:39).

Da Hausawa suka aro kalmar, sai suka ƙara faɗaɗa mata ma'anarta, ta ƙunshi duk wani nau'in aikin da za a yi don samar da wani abin biyan buƙata, domin a sauƙaƙa wa kai don biyan wasu buƙatun rayuwa; ko da kuwa ta hanyar yin kalamai ne da fatan baƙi, watau ta hanyar ƙirƙirar zantuka a cikin fasaha da azanci bisa wata daidaitacciyar ƙa'ida ko tsari, muddin dai za a samu biyan buƙata.

**5.0 Sana'o'in Gargajiyar Hausawa a Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi**

Sana'o'in Gargajiyar Hausawa sun kasance ɗaya daga cikin tubalan da makaɗa Kassu Zurmi ya yi amfani da su wajen gina wasu daga cikin ɗiyan waƙoƙinsa. Wannan matsayi da sana'o'i ke da, shi ya fayyace irin gurbin da suke da shi a cikin waƙoƙin nasa. Kassu Zurmi ya taka rawa ƙwarai wajen fito da nau'in sana'o'in da Hausawa ke yi don tallafa wa kawunansu wajen gudanar da harkokinsu na yau da kullum. Sana'o'in da Kassu Zurmi ya hasko sun kasance sana'o'in da Hausawa suka gada tun daga kakanni, kuma yana da matuƙar wahala a iya hasashen lokacin da Hausawa suka fara yin su. Masana sun bayyana cewa sana'o'in sun samu ne tun daga lokacin da Hausawa suka fara kafa matsugunnai don gudanar da rayuwa. Koma dai mene ne gaskiyar lamarin, Hausawa sun fara gudanar da waɗannan sana'o'in tun farkon kafuwarsu a wuri ɗaya don tallafa wa kawunansu ta fuskar tattalin arziki. Wannan matsayi da sana'o'i suka samu a cikin ayyukan fasahohin Kassu Zurni, ya taimaka wajen taskace su tare da bayyana su a matsayin sana'o'in da suke da asali a ƙasar Hausa. Ga wasu daga cikin sana'o'in da suka riƙa gilmawa a cikin wasu waƙoƙin Kassu Zurmi tare da nazartar saƙonnni da ɗiyoyin waƙoƙin suke ɗauke da su.

[4] Hira da aka yi da Dakta Muhammad Lawal Abdulƙadir, Malami a Sashen Nazarin Harshen Larabci, Jami'ar Jihar Kaduna, a ofishinsa da ke cikin makarantar, 22-05-2021.

## 5.1 Noma

Sa'id (2006:359) ya fassara noma da, "Kartar ƙasa da fartanya don raba shuka da haki." Ya kuma ƙara bayyana noma da, "Sana'ar shuka amfanin gona don ci ko sayarwa." Idan aka dubi waɗannan ma'anonin da Sa'id ya bayar za a fahimci cewa, duk wani nau'in aikin da za a yi don gyara ko sa ƙasa a yanayin da abin da aka shuka zai wala da samun sarari da zai samar da ingantacciyar yabanya, to shi ake ce wa noma. Kamar yadda masana suka faɗa noma na daga cikin sana'o'i na farko da Hausawa suka fara yi tun daga lokacin da suka fara kafuwa a wuri ɗaya don su rayu. Yanayin ƙasar Hausa ya ba mazaunan cikinta damar yin noma, kuma wannan hali na daga cikin abubuwan da suka jawo mutane daga sassa daban-daban na nahiyar ƙasashen baƙaƙen fata da ma maƙwabta na nesa da ƙasar Hausa. Kassu Zurmi ya yi amfani da fasaloli da kuma sauran abubuwan da sana'ar ta ƙunsa wajen gina wasu ɗiyan waƙoƙinsa, domin ya isar da saƙonninsa a sauƙaƙe. A iya cewa, ya fito da sana'ar noma a fili, musamman abubuwan da sana'ar ta ƙunsa da ma yadda ake gudanar da ita a ƙasar Hausa. Ya ta kawo bayanai kan noma a wurare da dama a cikin waƙoƙinsa. Ga misali wani ɗan waƙa nan a cikin waƙar da Kassu Zurmi ya yi wa wani Ɗanjijji, inda ya kawo hoton yadda ake gudanar da sana'ar a fili.

Jagora: Ɗanzuru karen Magaji tsohon doki,
: Bai gaji da gudu ba karkara taƙƙare,
: To bana Ɗanguru damana ta so ku,
: Bana ko kun yi ƙoƙari Ɗanjijji,
: Lalle na Mune kun ɗau taki,
: Udawa sun daɗe cikin **gonakku**,
: Na ishe shanun Dabai uban Ɗankawu,
: Suna ciki sun yi wata,
: Kun yi **turbe**,
: Kun yi kun maimaice hatci sun kama,
: **Turbe** kun maimaice hatci sun kama,
: Bana dai kun yi ƙoƙari Ɗanjijji,
: Bana dai kun yi ƙoƙari Ɗanjijji,
: Tun da kun samu dame guda da kyat ku shidda,
: Hak kau zaci sukai hatci sun kyawo.

Idan aka dubi wannan ɗan waƙa za a ga yadda Kassu Zurmi ya fito da cikkakken hoton yadda Hausawa suke gabatar da ayyukan noma tun daga farkon damana har ya zuwa ƙarshenta. A cikin ɗan waƙar, makaɗin ya ambaci yadda ake fara gyara gona tun kafin saukar ruwan farko, kamar barin tumakai da ya kira da udawa a gonakai don samar da taki. Ba tumakai kaɗai kamar yadda ya ambata a cikin ɗan waƙar ba, akan bar shanu su yi kiwo na tsawon lokaci a gonaki ga waɗanda suke da ikon haka don samar da isasshen takin da zai haɓaka tare da gyara ƙasar gonar don a sami yabanya mai yawa. Dukkan waɗannan shirye-shirye akan yi su ne tun kafin saukar ruwan sama. Bayan wannan hanyar ta samar da taki, akan kai taki gona a zuba don ya game ko'ina na gonar. Bayan nan akan yi noman farko bayan ruwan sama ya samu, kuma Kassu Zurmi ya kira irin wannan nau'in noman da turbe a cikin ɗan waƙar. Haka dai ya ci gaba da bayyana yadda ake aiwatar da gyaran gona tun kafin saukar ruwan damina har ya zuwa lokacin damina. Bayan nan, ya bayyana yadda ake girbe kayan amfani a ƙarshen damina, watau lokacin kaka. Makaɗin ya kawo waɗannan bayanan ne a cikin shaguɓe, watau yana yi wa Ɗanjijji

wanda yake yi wa waƙar gugar zana, yana nuna duk da ƙoƙarin da ya yi tun kafin damina har ya zuwa ƙarshenta da ƙyal shi da 'yan tawagar tasa suka haɗa dame guda.

**5.2 Farauta**

Sa'id (2006:135) ya fassara kalmar farauta da,"Yawon harbi ko kama naman daji." Wannan ma'ana da Sa'id ya bayar yana ƙoƙarin bayyana farauta da ƙoƙari neman naman daji a daji. Wannan sana'ar na daga cikin sana'o'in da ke samar da abinci kai tsaye. Haka kuma ya ƙara bayyana kalmar da," Fafutukar neman wani abu." Idan muka dubi wannan fassara, za mu fahimci cewa, an danganta kalmar da hanyar nema. A wannan bagiren za mu ɗau ma'anar farko, domin ita ce ta yi daidai da abin da za a yi nazari a nan. Sana'ar farauta ita ce sana'a ta farko da ɗan'adam ya fara yi a bisa doron ƙasa tun kafin kafuwar mutane a wuri ɗaya, domin su rayu (Gusau, 2003). Makaɗi Kassu Zurmi ya yi amfani da tsari da yanaye-yanayen farauta wajen gina tare da tsara waƙoƙinsa. A iya cewa, kaso mafi yawa na waƙoƙin da ya yi duk a kan farauta ne, shi ya sa ake kiran sa da makaɗin farauta. Ya yi wa mafarauta da dama waƙa, kuma a lokacin da yake raye da shi ake fita farauta. Ga wasu ɗiyan waƙar da ya yi wa Ɗammamu Kore nan inda ya fito da shirin da 'yan farauta ke yi tun kafin su shiga daji:

Jagora : Hay yau ba su huce ba Galadawa,
: Sai sun koma aibin **hwarautai**,
: Hay yau ba su huce ba Galadawa,
: Sai sun koma aibin **hwarautai**.

Jagora : Ko Kassuwa kag gane su,
: Kana ganin masu niyya,
: Kowane kulki da gora gare shi,
: Da mugunyaw wuƙa tai ga gutsu,
: Da ganin babu takobi shina nan sullace,
: Ya bi cinya da taggo.

Jagora : Ba saye ba sayawwa,
: An dai tahi Kassuwa ba na nono,
: Ba saye ba sayawwa,
: An dai tahi Kassuwa ba na goro,
: An dai zo don bidaz zanga-zanga,
: Don wata yat tijara ta tashi.

A cikin ɗiyan waƙar da Kassu Zurmi ya yi wa Ɗammamu Kore, ya kawo cikakken hoto na yadda yan farauta suke kasancewa a yayin da suka yi shiri suka ɗau makamai na shiga daji don farautar namaun daji, wanda da ganin su an san ba cin kasuwa za su ba. Waɗannan makamai da suke ɗauka ba farauta kaɗai suke yi da su ba, har da kare kai. Bisa ga al'adar 'yan farautar ƙasar Hausa, watau mafarauta kan gwabza da junansu a daji musamman waɗanda suke da tsohuwar tsama da juna. Wannan fage yana ba waɗanda suke da tsama da juna damar su goge rainin da yake a tsakaninsu. A wasu lokutta naman dajin da aka kashe ne ke haddasa faɗa a tsakanin mafarauta. A inda kowane mafarauci zai yi ƙoƙarin ɗibar nasa Kason, wanda a ƙarshe wannan yanayi na rikiɗiwa ya koma tarzoma, inda za su ta amfani da makaman da makaɗi Kassu Zurmi ya zayyanu a cikin ɗiyoyin waƙar da ta gabata, irim su, wuƙa da gora da takobi da kuma kulki wajen yaƙar kawunansu.

Bayan waɗannan ɗiyan waƙar, akwai wani ɗan waƙar da makaɗin ke bayanin irin raunukan da mafarauta ke ji wa kawunansu a yayin da suke gwabza faɗa. Harkar farauta wani faffaɗen fage ne da ke ɗauke da tarin abubuwa da suka shafi sana'ar, wanda hatta raunukan da ake samu na da sunayen da su mafarautan ke kiran su da su. Misali a cikin waƙar da Kassu Zurmi ya yi wa Labbo na Magaji, wanda a cikin ɗan waƙar ya fito da irin raunukan da mafarauta kan samu a yayin da suka shiga daji. Ga abin da Kassu Zurmi ke cewa:

Jagora: Tun daga wagga Lamba ta gabas,
: Yaro dantce hag ga lambay yamma,
: In kag ga rijiya ga baya,
: 'Yan Jabanda nay yasa ta,
: Ko tsayin wata gun goshi,
: Kun san tsayin wata?
: Saran goshi irin na Nagunda,
: Shan doguwa da takobi,
: Labbo saran ƙwanda hannu ya birkice ba aiki,
: Su ba Allah su ba musakkan kansu,
: Rijiya bisa baya kau,
: Saran allo irin na Annen Dayau,
: 'Yan Jabanda sun ɓata shi.

Idan aka nazarci wannan ɗan waƙa, za a ga makaɗin ya fito da nau'ukan raunukan da mafarauta ke samu a yayin da rikice ya barke a daji. Ya yi amfani da kalmar rijiya wadda take alamta raunin da ake yi wa mafarauci a gadon baya. Haka kuma, ya yi amfani da tsayin wata da raunin da ake yi wa mutum a goshi. Ya yi amfani da shan doguwa da takobi da saran ƙwandan hannu. Waɗannan kalmomi da makaɗin ya kawo ya ƙara fito da sana'ar farauta a matsayin wata duniya wadda ke ɗauke da abubuwa da yawa. Tarin kalmomin fannu da mafarauta ke amfani da su ya tabbatar da faraauta a matsayin makaranta da wani ba zai iya shiga harkar kai tsaye ba, watau sai ya bi waɗanda suka san abin, kuma ya koya sannan zai iya shiga a yi da shi. Makaɗin ya yi amfani da ire-iren waɗannan kalmomi wajen gina waƙarsa tare da jan zaren tunaninsa tun daga farko har ya zuwa ƙarshe.

## 5.3 Su

Sa'id (2006:399) ya fassara kalmar su da, "Farautar kifi a ruwa." Kamar yadda bayanin ya nuna, su aikin ne na farautar dabbobin da ke rayuwa a cikin ruwa, musamman kifi. Wannan tsohuwar sana'a ce da Hausawa suka gada, kuma sana'a ce mai asali a ƙasar Hausa. Hausawa a da kan yi la'akari da wurin da ke da ruwa, domin sha da kuma gudanar da sana'ar su kafin su kafa gari (Gusau, 2003:5). Makaɗi Kassu Zurmi ya fito da wannan sana'ar a wurare daban-daban a cikin waƙoƙinsa don tabbatar da ita cikin sana'o'in da wasu Hausawa ke yi. Haka kuma, sana'a ce ta samar da abinci kai tsaye, wanda masu yin ta ke dogarau da ita wajen ci da sha da kuma biyan wasu buƙatu na rayuwa. Sana'a ce da ta ƙunshi 'yan gado da kuma 'yan haye, kuma ba a shigar ta kai tsaye, sai an koya daga ahalinta. Sana'ar su sana'a ce da ke da tarin sirraka da dole sai mai koyo ya kwantar da kai ya yi biyayya, sannan a buɗa masa sirrikanta. Ga wani misali a cikin ɗan waƙar da Kassu Zurmi ya yi wa wani shahararren ɗan tauri mai suna Shaho Bagobiri:

Jagora : Dole a bar wa dorina gabatar gulbi

: **Su** in ya ɓaci,
: Sai ɗiyan **sarkawa**,
: Yaro koma gehe kada,
: Kadannu su kashe ka.

A nan Makaɗi Kassu Zurmi yana ƙoƙarin bayyana wanda yake yi wa waƙar da wani mashahuri, wanda wani aikin in ya ɓace sai su ka iya shiga don su daidaita shi. A wajen ƙoƙarin kambama shi gwaninsa ne ya yi amfani da ɗiyan sarkawa waɗanda suke gwanaye a farauta ta cikin ruwa. Idan ruwa ya kawo ya kai wani matakin da ba kowa ke iya shiga ba, to a kan nemi 'ya'yan sarkawa don su kaɗai ke iya tunkarar ruwan, su shiga, kuma su gabatar da dukkan ayyukansu ba tare da wata fargaba ko tsoro ba. Akwai masu sana'ar su da ba za su iya gabatar da sana'ar tasu a ruwan da ke da kadoji ko dorina ba, domin su waɗannan namun ruwan sai masunta da suka ƙasaita, watau ba kowane masunci ke iya gabatar da sana'arsa a cikin irin gulabe ko kogunan ba. Haka kuma, ba hannu biyu sarkawa suke ba, domin suna da shiri na musamman da ke ba su zarafin yin duk abin da suke muradi a cikin ruwa. Irin waɗannan darajojin ne makaɗin ya ba gwaninsa a fagen tauri da kuma farauta. Wannan tsari da makaɗin ya ɗauko na siffanta wasu sana'o'in Hausawa a cikin waƙoƙinsa da abin da yake son mutane su fahimta, ko kawo masu hoton wani lamari a cikin zukatansu, shi ne ya ƙara fayyace gurbin da sana'o'in gargajiyar Hausa ke da shi a cikin waƙoƙinsa. Har ila yau, ya taimaka wajen kawo su a matsayin sana'o'in da ke da tushe da asali a ƙasar Hausa. Bugu da ƙari, ya yi amfani da su wajen gina tubalai na waƙoƙinsa.

### 5.4 Sussuka

Sa'id (2006:403-404) ya bayar da ma'anar sussuka da,"Aikin daka zangarkun hatsi don raba shi da ƙaiƙayi." Wannan tsohuwar sana'a ce da Hausawa ke yi, kuma ta mata ce. An fi yin wannan sana'ar bayan an girbe kayan amfanin gona, kuma a waje ake gudanar da ita. A wasu lokattu gungun mata ne ke haɗuwa su yi ta dakan hatsi don ƙoƙarin raba ta ƙaiƙayi. Bayan sun raba ta da ƙaiƙayin sai su sheƙe ta don fitar da tsaba kaɗai. A da akan biya masu sussukan ne da tsabar hatsi, amma da zamani ya shiga sai aka koma yin ciniki don biya da kuɗi. Har ila yau, akan iya gudanar da wannan sana'ar a kodayaushe. Makaɗin Kassu Zurmi ya ambaci wannan sana'ar a cikin waƙar da ya yi wa Ɗanjijjiki.

Jagora: Ibilishin **masussuki**,
: Ɗanjijjiki da kai ne mai koda nag gani tar ruɗe.
Jagora : Ka daɗe kana satah hwage ana kokowa,
: Amma sun sanad da kai,
: Sun ce ba mu yi da shi tsoho ne,
: Ga idon kama an ƙona.

A cikin wannan ɗan waƙar makaɗin bai ambaci sana'ar kai tsaye ba, sai dai ya kamanta gwaninsa da aljanin masussuka, watau aljanin da ke ba masussuka tsoro a yayin da suke gudanar da sana'ar. Duk da cewa ba masu sana'ar ya nufa kai tsaye ba a cikin ɗan waƙar, amma ya kawo hoton sana'ar, kuma ya danganta ta a matsayin wadda Hausawa ke yi don neman na kansu. Wannan yanayi ya ƙara tabbatar da yadda makaɗin yake amfani da sana'o'in gargajiyar Hausawa wajen ƙulla zaren tunanin waƙoƙinsa. Hausawa mutane ne masu sana'a, kuma amfani da sana'o'in gargajiya wajen gina zantuka na waƙoƙinsa kan iya taimaka wa saƙonnin da makaɗin ke son ya isar, su kai ga jama'a ba tare da matsala ba. Haka kuma, suna zama hanya ta fito da hoton abubuwa a cikin sauƙi ba tare da an yi dogon bayani ba.

## 5.5 Kiwo

Sa'id (2006:247) ya fassara kalma kiwo da, "Renon dabbobi." Kiwo sana'a ce da Hausawa suka gada tun daga lokacin da suka fara share wuri don zama na din-din-din ko na wucin gadi, musamman idan rai ya natsu da wurin. Hausawa kan kiwata nau'ukan dabbobi da tsuntsaye da dama kama daga awakai da dabbobi da kaji da zabbi da sauransu. Maƙi yawan dabbobin na gida ne, kuma ci ake ko a sayar idan buƙatar haka ta tashi. Haka kuma, a gida ake kiwata su, sai dai akwai kare wanda Hausawa ke kiwatawa, amma ba don su ci ba, sai dai su yi amfani da shi a wajen tsaron dukiya, ko kuma farauta. Baya ga kare, akwai dawakai da jakuna, waɗanda Hausawa ke kiwatawa, su ma ba don a ci ba, sai don amfani da su a wajen ɗaukar kaya da kuma tafiye-tafiye. Mata su suka fi taka rawa a wajen kiwata dabbobin gida, domin su ke zaune a gida a kodayaushe. Kiwo na daga cikin hanyoyin da Hausawa ke amfani da su wajen ƙarfafa tattalin arziƙinsu da na iyalinnsu. Babu gidan da za a je a rasa dabbar da 'yan gida ke kiwatawa, kuma hanya ce wadda ake ɗora yara don su tashi da tattali da kuma neman na kai. Makaɗi Kassu Zurmi ya yi amfani da wannan kalma ta kiwo a wuraren daban-daban a cikin waƙoƙinsa wajen ƙoƙarin cusa wasu saƙonni a zukatan masu saurarונsa. An ga a wata waƙa inda ya yi ƙoƙarin nuna yadda Hausawa ke da al'ada irin ta aje tsuntsaye a gida don kiwo. Misali a waƙar Shayi ɗan gidan Labbo ya fito da wannan hoto a sarari:

Jagora: Kakab bana tai kyawo,
: Ko ta bara mun gode,
: Sai dai Sha-yaya bai yi komi ba,
: Na ga 'yan tantabaru cikin ruhewassu,
: Tantabaru goma,
: Amma yanzu ba su sun ƙare,
: Yanzu kam saura nai guda baƙi namiji,
: Ko shi kam dan yana yi mai waƙa,
: Inda swahiya taw waye ya ɗora mabanci.

Makaɗa Kassu Zurmi ya fito da yadda Hausawa ke kiwon tsuntsaye a gidajensu, kuma wannan asali ya samo tun lokacin da suka fara share wuri, domin zama. Wannan tsari ne na tattalin arziƙi na matan Hausawa, kodayake ana samun wasu maza da ke kiwo a gidajensu. Bisa ga al'ada mata aka fi sani da kiwon irin su kaji da sauran dabbobin gida da ake kiwata a muhallan zaman mutane. Idan muka dubi ɗan waƙa na sama, za mu ga makaɗin ya yi bayanin yadda ake kiwata tantabaru a gidan su Shayi. Kawo hoton yadda ake kiwata tantabaru a ruhewassu, watau rumbuna, shi ya tabbatar da irin wannan nau'in kiwon da Hausawa ke yi, musamman wanda mata ke yi a gidajen aurensu. Kodayake ya kawo wannan ɗan waƙar ne wajen yi wa gwaninsa zambo, watau Shayi ɗan gidan Labbo, amma ya yi ƙoƙari ƙwarai wajen fito da ire-iren sana'o'in gargajiya da Hausawa ke yi, waɗanda suke tallafa wa tattalin arziƙinsa.

## 5.6 Fawa

Sana'ar fawa daɗaɗɗiyar sana'a ce da aka san Hausawa da ita tun tsawon lokaci. Kwarewar da Hausawa suka yi a kan iya fiɗa da gyara nama shi ya tabbatar da su a matsayin gwanaye da za su iya goga kafaɗa da kowace irin al'umma a duniya. A dukkan faɗin ƙasashen baƙaƙen fata babu al'ummar da ke da fasahar gyara da feɗe dabba irin ta Hausawa. Hausawa ne a dukkan ƙasashen Afirka ke iya fid da fatar dabba daga jikinta ba

tare da sun illata ta ba. Haka kuma, sukan iya raba tsoka da ƙashi da kuma kayan cikin dabba da sauran sassanta a tsanake ba tare da wahala ba. Sa'id a cikin ƙamusunsa (2006:138) ya bayyana ma'anar fawa da, "Sana'ar sayar da nama." Idan aka yi duba da wannan ma'ana za a fahimci cewa sana'ar fawa ita ce sana'ar sayar da nama. A ƙasar Hausa, duk mai fiɗa da gyara nama tare da sayar da shi, to, shi ake kira da mai sana'ar fawa. Gudanar da sana'ar gaba ɗaya, ita ce ake cewa fawa, amma su masu gudanar sana'ar su ake kira da rundawa. Makaɗi Kassu Zurmi ya kakkawo batutuwan da suka jiɓanci wannan sana'ar ta fawa a wurare da dama a cikin waƙoƙinsa. Wannan ba zai zama abin mamaki ba, domin kakan Makaɗi Kassu Zurmi barunje ne, kuma har sarautar sarkin fawa ya yi a Dunfawa, watau garin da ya zauna ya rayu har ya koma ga Allah. Ba wani abin mamaki ba ne idan aka fiye ganin gilmawar hotunan sana'ar fawa a cikin waƙoƙinsa, kuma ya yi amfani da yanaye-yanayen sana'ar wajen gina waƙoƙinsa. Ga wani misali nan daga wani ɗan waƙar da ya yi wa Ɗammamu Kore.

Jagora: Dauri na ce ku daina, kad ku fara,
: Kai ko yau in sunka ƙara ku ƙara,
: In sunka koma ku koma,
: A iske mutum da gora a hyaɗe,
: A take a yanke,
: **Sarkin hwawa** shi kau ya heɗe,
: **Sarkin hwawan** daji Amasa,
: **Sarkin hwawan** garinmu.

A cikin wannan ɗan waƙa, makaɗin ya yi amfani da salo irin na zuga inda ya yi ƙoƙarin yin hani ga wani lamari tare da ingiza wasu da su ɗau mataki na ramuwa. Makaɗin ya yi amfani da wasu kalmomi da ke da alaƙa da sana'ar fawa, kamar su "yanke" da "heɗe" a cikin ɗan waƙar. Ita wannan kalma ta heɗe kamar yadda ya ambace ta a cikin ɗan waƙar tana nuni ne da wani nau'in gyara da rundawa suke yi wa dabbar da suka yanka, watau sukan yi ƙoƙarin feɗe ta don su cire fata daga jikinta, sannan su fid da namanta tare da sauran sassanta ga masu mabuƙata. Haka kuma, ya ambaci Sarkin Fawan garinsu, wanda idan aka yi duba da kyau, za a fahimci cewa bayan kasancewarta sana'ar da Hausawa ke yi, kuma tana tsarin shugabanci. Kawo wannan batu na tsarin shugabanci da sana'ar ke da shi, shi ya ƙara tabbatar da ita a matsayin sana'ar gargajiyar Hausawa. Har ila yau, Makaɗin ya sake hasko sana'ar kai tsaye a cikin wani ɗan waƙar da ya yi wa Labbo na Magaji. Ga abin da yake cewa:

Jagorsa: Kuru abin kiɗan 'yan'anna,
: Gangumma a wa basarai,
: Na a wa **rundawa**,
: Jauje a kiɗa ma Anna bori.

Makaɗi ya yi amfani da salon kamancen daidaito a inda ya yi amfani da kalmar rundawa wadda take suna ne da ake kiran mahauta da shi, watau masu gyara da sayar da nama. Bayyanar wannan suna na masu sana'ar sayar da nama shi ya ƙara nuna yadda makaɗi ya yi ta ƙoƙari wajen fito da sana'o'in gargajiyar Hausawa a cikin waƙoƙinsa. Makaɗi Kassu Zurmi ya gina mafiya yawan waƙoƙinsa ta amfani da sigogin sana'o'in Hausawa da dama don fito da saƙonninsa a sarari. Haka kuma, makaɗin ya fi alaƙantuwa da wannan sana'ar

ta fawa fiye da sauran sana'o'in da ya kawo a cikin waƙoƙinsa. Ana iya kiran sa da ɗan gado don gadon sana'ar fawa ya yi daga wajen kakansa, wanda shi ya sa ya yi ta kawo wasu muhimman batutuwan sana'ar a cikin wasu waƙoƙinsa. Har ila yau, makaɗin ya nuna yadda sana'o'in gargajiya ke da matuƙar muhimmanci a ƙasar Hausa, kuma suna daga abubuwan da ake lura da su wajen ware mutanen kirki da kuma ɓata gari. Haka kuma, a cikin ɗa na wata waƙa da makaɗin ya yi wa wani mahauci mai suna Garba, ya fito da yadda ake aiwatar da sana'ar duk da a cikin zambo ya kawo batun, amma ɗan waƙar ya ƙara jaddada abin da ake ƙoƙarin fayyacewa. Ga abin da yake cewa nan a cikin waƙar:

Jagora: Mai son banza sai ya wuce,
: Garba za ya yankan salla tahi,
: Ka ga sisi da ahu ka yi tukunya cike.

Ɗan waƙar ya kawo batu wanda ya shafi rundawa, watau mahauta waɗanda suke sayen dabbobi su yanka, musamman a lokacin salla, sannan su sayar da naman bayan sun gyara ga mabuƙata. Wannan yanayi yana nuna yadda mahauta ke samun kansu a duk lokacin da bikin salla ya matso inda za a ga suna ta fafatukar neman abin yankawa, domin biyan buƙatar mutane. A cikin zambo ya kawo wannan batu, amma saƙon ya isa, kuma an ga yadda ya yi amfani da yanaye-yanayen sana'ar wajen gina ɗan waƙar.

**5.7 Kira**

Kalmar ƙira kamar yadda Sa'id ya fassara ta a cikin Kamusun Hausa (2006: 281), na nufin," Narka ƙarfe da sarrafa shi don samar da ma'aikaci kamar fatanya ko garma." Wannan ma'ana na nuni da yadda sana'ar ke samar da kayan aiki bayan an narkar da ƙarafa. Sana'a ce daɗaɗɗa a ƙasar Hausa, kuma tana taka rawa wajen tafiyar da sauran sana'o'in da Hausawa suke gudanarwa a garuruwansu. Sana'ar ƙira na da dangantaka ta ƙut-da-ƙut da sauran sana'oin gargajiyar Hausawa. Kasancewar dogarau da sauran sana'o'in gargajiyar Hausawa suke yi da ƙira shi ya sa ake ganin da wuya su iya motsawa ba tare da taimakon maƙera ba. Abin nufi idan har maƙera suka kasa sauke nauyinsu na samar da kayayyakin aikin ga sauran masu sana'o'i, lalle haka na iya haifar da cikas gare su. Makaɗi Kassu Zurmi ya ambaci masu gudanar da sana'ar sarrafa ƙarfe a wasu sassa da dama a cikin waƙoƙinsa. Akwai wuraren da ya kawo su kai tsaye a cikin waƙoƙinsa, kuma akwai inda ya kawo su a kaikaice a wasu ɗiyoyin waƙoƙinsa. Kamar yadda ya yi amfani da yanaye-yanayen wasu sana'o'in wajen gina waƙoƙinsa, haka ya yi amfani da ƙira wajen gina wasu daga cikin sigogin ayyukan fasaharsa. Sana'ar ƙira kamar yadda ayyukan Kassu Zurmi suka nuna, suna daga cikin jerin sana'o'in Hausawa na asali. Saboda muhimmancin sana'ar ne a da ya sa, Hausawa suke yin la'akari da wuraren da suke da yalwar duwatsu don samun tama da ake sarrafawa ya zuwa ƙarafe a sauƙaƙe.

A cikin waƙar da Makaɗi Kassu Zurmi ya yi wa wani maƙeri mai suna Mani na Maƙera, an ga inda ya zayyanu zantuka da suka shafi sana'ar ƙira a cikin waƙar, kuma wannan ya ba shi damar fito da abubuwan da suke cikin zuciyarsa. Wannan ba wani sabon batu ba ne, domin makaɗin ya ƙware wajen amfani da sigogin sana'o'in gargajiya wajen gina waƙoƙinsa. Ga wani ɗan waƙa nan da aka tsakuro daga cikin waƙar Mani na Maƙera:

Jagora: Barkak ka da gaba Mani,
: Taho jikan zaki bari tsoron arna,
: Hwaɗa ma **Maƙera** ina bankwana,
: Ban dai rena ma kiran Nani ba,
: Da niz zo wadda akai duy yai man,
: Zaman doki da ƙahwahu yai man.

Idan aka yi duba da idon nazari, za a ga ɗan waƙar na ɗauke da wasu salailai na zuga da nuna asali da kuma kwatanci. Haka kuma ya nuna godiyarsa bisa ga alherin da gwaninsa ya yi masa a cikin ɗan waƙar. Ya yi amfani da su ne don fito da saƙonninsa tare da isar da su a cikin sauƙi. Ambaton kalmar maƙera da ya yi a cikin ɗan waƙar, ya fito da muhimmanci da kuma wanzuwar sana'ar ƙira, kuma ya tabbatar da ita a matsayin sana'ar gargajiyar da Hausawa suke yi. Bisa ga al'ada, Bahaushe na amfani da sunayen sana'o'i wajen laƙaba wa masu gudanar da ita. Wannan lamari shi ya faru ga Mani na maƙera, wanda da ji an san ya shafo sana'ar ƙira. Bayyanar wannan laƙabin suna mai nasaba da sana'ar ƙira, shi ya ƙara fito da yadda makaɗin ya yi ta amfani da bayanan sassa da dama na sana'o'in gargajiyar Hausawa wajen samar da tubalai da ya yi amfani da su wajen gina ilahirin waƙoƙinsa.

## 5.8 Awo

Sana'ar awo sana'a ce ta Hausawa wadda ta samo asali tun da daɗewa. Ana iya sa ta a cikin rukunan sana'o'in da ba su kai sana'o'i irin su ƙira da noma tsufa a ƙasar Hausa ba. Sana'o'i ne da suka samu bayan juyin zamani da Hausawa suka samu, domin kamar yadda aka sani, ba lalle sai haɗuwa da baƙi ke sa al'adun mutane su sauya ba, watau ita kan ta al'adar tana iya sauyawa, saboda tsawon lokaci. Wannan abu na sauye-sauyen lokaci da kuma yanayi na tattalin arziƙin al'umma shi ya tsirar da yin awo, wanda a ƙarshe ya haifar da waɗanda suka mayar da ita sana'a. Kamar yadda bayanai suka tabbatar, kowane Bahaushe shi ke noma abin da za ya ci na tsawon shekara. Yakan zama abin kunya idan har ya zamana mutum ba zai iya noma abincin da za iya ci na tsawon shekara ba. Sa'id (2006:22) ya fassara awo da," Gwaji." Ita wannan kalmar ta awo tana nufin gwaji, amma bisa ga ɗabi'ar harshe ana samun yanayin da kalmomi ke sauyawa ta fuskar ma'ana, watau ko dai su samu ƙarin ma'ana ko ma'ana ta faɗaɗu ko ma ta canza gaba ɗaya. Abin da ya faru ga kalmar awo ke nan, ta samu wata ma'ana da ta saɓa wa ma'anarta ta asali, sai ta kasance tana bayyana wata sana'a da wasu mutane suke yi ta hatsi.
Makadî Kassu Zurmi ya yi amfani da wannan kalmar a cikin wata waƙa da ya yi wa Gagarau na Magaji inda ya yi ƙoƙarin amfani da ita don ma'anarta ta fito a fili. Duk da ba sana'ar ya nufa kai tsaye ba, amma ya tasirintu da sana'ar, musamman idan aka yi la'akari da yadda ya yi amfani da sunan sana'ar wajen fayyace abin da yake son a fahimta a cikin waƙar. Ga yadda ya saƙo kalmar nan a cikin ɗan waƙar da ya yi wa Gagarau na Magaji:

Jagora : Ko da mai **awon** sunanai,
: Ya ja kasagaren Bawa,
: Baba ɗan namijin Zaki.

Amfani da kalmar da mkaɗin ya yi a cikin ɗan wannan waƙar, ya nuna irin gudummuwar da yake bayarwa ta fito da sana'o'in gargajiyar Hausawa. Ya yi amfani da salon nuna yadda gwaninsa ya gagara ne, kuma a lokaci ɗaya ya saƙa kalmar awo don jaddada ƙasaitar wanda yake wasawa a cikin ɗan waƙar. Sanin yanaye-yanayen sana'o'in shi ya bayar da dama makaɗin ya riƙa wasa da kalmomin yadda yake buƙata ba tare da matsala ba, kuma yana yin haka ne don cusa wani tunani a zukatan masu sauraro don saƙon ya isa ba tare da wata wahala ba. Haka kuma, wannan ya ƙara tabbatar da makaɗin a matsayin wanda yake da cikakkiyar masaniya a kan kalmomin fannu da suka shafi sana'o'in gargajiyar Hausawa.

## 6.0 Sakamakon Bincike

Wannan takarda ta gano wasu fitattun abubuwa da suke zaman sakamakon binciken da aikin ya gano. Sakamakon bincike dai wasu abubuwa ne da ake ganowa bayan an kammala binciken da aka gudanar, kuma suna zaman ƙari ta fuskar ilimi da aka samo a dalilin aikin da aka yi. Ga abubuwan da aka gano nan kamar yadda za a gani:

Binciken ya gano yadda Makaɗi Kassu Zurmi ya yi amfani da sigogin sana'o'oin gargajiyar Hausawa a wurare da dama wajen gina tubalan da ya yi amfani da su wajen gina waƙoƙinsa. Wannan ya tabbatar da gudummuwar da makaɗin ya bayar wajen bunƙasa adabin Hausawa.

Binciken ya daɗa gano yadda Hausawa suke darjanta sana'o'insu na gargajiya, kuma shi ya sa ake yawan jin su a cikin maganganunsu na yau da kullum tare kuma da cin karo da su a cikin ayyukansu na fasaha.

Binciken ya taimaka wajen gano sana'o'in da suke da asali da tushe da ƙasar Hausa da kuma yadda suka mamaye wani muhimmin gurbi a cikin waƙoƙin Kassu Zurmi, kamar dai yadda ayyukansa suka nuna.

## 7.0 Kammalawa

Wannan takarda ta dubi gurbin da sana'o'in gargajiyar Hausawa suke da shi a cikin waƙoƙin Makaɗi Kassu Zurmi. An kawo yadda sigogin sana'o'in Hausawa suka taimaki makaɗin wajen gina tubalan da ya yi amfani da su wajen ƙulla zaren tunaninsu a wurare da dama a cikin waƙoƙinsa. Wannan fasaha da Kassu Zurmi ya nuna na sarrafa batutuwan da suka shafi sana'o'in ya taimaka wajen fito da wasu fitattun sana'o'in gargajiyar da Hausawa ke yi, kuma ayyukan fasaharsa sun tabbatar da su a matsayin sana'o'in da ke da asali a ƙasar Hausa. Har ila yau, a cikin taƙaitaccen tarihin da aka kawo na Kassu Zurmi an nuna cewa kakansa mahauci ne, kuma har sarautar sarkin fawa ya yi a lokacin da yake raye. Wannan ya nuna shi ma ya gaji ɗaya daga cikin sana'o'in da ya yi ta amfani da sigoginss wajen gina waƙoƙinsa.

## Manazarta


Alhassan, A. da wasu. (1988). *Zaman Hausawa*. Lagos: Academy Press Limited.

Asiru, A. (2009). "Sutura Adon Jiki: Sana'ar Ɗinki da Ci Gabanta a Kasar Kano." Kundin Digiri na Uku. Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Asiru, A. (2017). *Sana'ar Dinki da Ci Gabanta*. Zaria: Ahmdu Bello University press Limited.

Auta, A.L. (2006). "Tattalin Arzikin Al'umma: Nazarin Sana'o'i da Kasuwancin Hausa. *Algaita Journal of Current Research in Hausa Studies,* No 4 Vol.1.

Garba, C.Y. (1991). *Sana'o'in Gargajiya a Kasar Hausa Spectrum.* Ibadan: Books Ltd.

Gusau, S.M. (2003). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka. Kano:* Benchmark Publishers Limited.

Ibrahim, U. (2011). "Tasirin Haye a Sana'o'in Hausawa na Gargajiya." Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Madabo, M.H. (1979). *Ciniki da Sana'o'i a Kasar Hausa*. Kano: Annuri Printing &Puplishing CO, D/Rimi, Bayan Gidan Sakwaya, R/Lemu.

Magaji, A. (2016). *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa*. Ibadan: Spectrum Books Limited

NNPC. (1968). *Labaru na Da da na Yanzu.* Zaria: The Northern Nigerian Publishing Company.

Rambo, R.A. (2018)."Nason Sana'ar Sassaƙa a Cikin Wasu Adabin Hausa". Bauchi*: Gadau Journal of Hausa Languages and Linguistics,* Bauchi State University Vol 1-2018.

Rimmer, E.M da Wasu. (1966). *Zaman Mutum da Sana'arsa*. Zaria: Northern Nigeria Publishing Company.

Ruma, A.K. (2016). "Sana'ar Saƙa Jiya da Yau a Ƙaramar Hukumar Batsari." Kundin Digiri na Ɗaya. Sashen Harsunan Nijeriya. Katsina: Jami'ar Umaru Musa 'Yar'adua.

Sa'id, B. da wasu. (2006). *Kamusun Hausa*. Kano: Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero.

Sallau, B.A. (2009). "Sana'ar Wanzanci da Sauye-Sauyen Zamani Jiya da Yau." Kundin Digiri na Uku. Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Sharifai, B. I. (1990). "Take da Kirarin Sana'o'in Gargajiya: Nazarin Ma'anarsu da Muhimmancinsa Ga Rayuwar Hausawa." Kundin Digiri na Biyu. Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Tukur, H. (2000). "Kafuwar Sana'ar Gurasa a Kano (Reshen Karamar Hukumar Dala)." Kundin Digiri na Ɗaya. Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Umar, S. S. (2008). "Sana'ar Bugu a Wasu Ɓangarori na Kasar Kano. Kundin Digiri na Ɗaya. Sashen Harsunan Nijeriya. Kano: Jami'ar Bayero.

Yahya, A.B. (1997). *Turken Nazarin Waƙa*. Kaduna: Ɗab'in Fisbas.

Yahya, A.B. (2016). *Salo Asirin Waƙa*. Kaduna: Ɗab'in Fisbas.

**HIRA**

| **Lamba** | **Suna** | **Shekarau** | **Wuri** | **Lokaci** | **Rana** |
|---|---|---|---|---|---|
| 1 | Malam Muhammad Ibrahim Ɗanmadamin Birnin Magaji | 47 | A gidan rediyo na Kaduna FRCN | Karfe 10 na safe | 31/03/2019 |
| 2 | Malam Muhammadu Sayaya | 38 | A gidan rediyo na Kaduna FRCN | Karfe 10 na safe | 31/03/2019 |
| 3 | Malam Suleman Abubakar | 60 | A gidansa da ke Unguwar Kofar Mata, Kano | Karfe 12 na rana | 06/06/2021 |
| 4 | Malam Mansur Abdullahi | 34 | Tudun Wada, Katsina | Karfe 4 na marece | 11/04/2021 |
| 5 | Dakta Muhammad Lawal Abdulƙadir | 51 | A ofishinsa da ke cikin Jami'ar Jihar Kaduna | Karfe 11 na safe | 22/05/2021 |

© Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto 